(١)

## FALALAR SHAHADA DA MATSAYIN SHAHIDAI DA FALSAFAR YAKI A MUSULUNCI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Shahidai suna da lada gami da haskensu ne a wurin Ubangijinsu)** [al- Hadid: 19]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai yin shahada wajen ɗaukaka kalmar Allah babban matsayi ne, manufa ce mai girma da daraja, wadda Allah Maɗaukakin Sarki ne yake zaɓar waɗanda suka cancance ta a cikin bayainsa, Allah mai girma yana cewa: **(Yana ɗaukan shahidai daga cikinku..)** [Ali Imran: 140], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Duk wanda ya yi wa Allah da Manzon Allah biyayya, to lallai waɗannan su ne suke tare da waɗanda Allah ya yi masu ni'imomi cikin Annabawa da Siddiƙai da Shahidai da mutanen kirki, lallai zama da waɗannan kam abu ne da ya yi kyau matuƙa..)** [an- Nisa'i: 69], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Da na yi burin a kashe ni wajen ɗaukaka kalmar Allah, sannan a raya ne, sannan a kashe ni, sannan a sake raya ni, sannnan a sake kashe ni, sannan a sake raya ni, sannan a sake kashe ni)**.

Shahidi na gaskiya shi ne wanda ya rasa rayuwarsa wajen ɗaukaka kalmar Allah, yana mai bai wa ƙasarsa, ko mutuncinsa,

ko dukiyarsa kariya, to lallai wannan ana gafarta masa zunubansa tun daga lokacin da ɗigon farko na jininsa ya ɗiga, zai kuma ga mazauninsa a aljanna, zai ceci mutane saba'in daga cikin danginsa, lallai babban cinikin da yake tsakanin shahidai da Ubangijinsu ciniki ne mai lamuni, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai Allah ya sayi rayukan muminai, da dukiyoyinsu daga gare su, akan lallai zai ba su aljanna, suna yaƙar waɗanda suka auka masu da yaƙi fisabililLahi, su kashe, a kuma kashe su, lallai Allah ya yi masu alƙawari na gaskiya a cikin littattafan Attaura da Injila da Alƙur'ani..)** [at- Tauba: 111], haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Na rantse da wanda rayuwa ta take hannunsa, ba za a taɓa ji wa wani rauni a hanyarsa ta ɗaukaka kalmar Allah ba –Allah kaɗai ya san wanda ake ji wa rauni dominsa- face ranar alƙiyama ya zo da launi irin launin jini, amma ƙamshinsa na almiski ne).**

Su Shahidai -duk kuwa da cewa sun bar wannan rayuwa da muke ciki-, lallai su rayayyu ne a wurin Ubangijinsu mai girma da buwaya, suna farin cikin da baiwarsa, suna kuma yi wa juna albishir da falalarsa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Kada ku taɓa zaton cewa waɗanda aka kashe akan hanyar Allah matattu ne, a'a, a raye suke, rayuwar da Allah ya bar wa kan sa sani, suna nan wurin Ubangijin su ana azurta su da arziki mai faranta rai da Allah ne kawai ya sani. Farin-ciki da murna sun lulluɓe fuskokin su sakamakon abin da Allah ya ba su na wasu abubuwa da aka keɓance su da su saboda falalar sa, suna kuma farin-ciki da murna da 'yan uwansun da suka bari a raye a duniya suna tsaye akan hanyar imani da jahadi, da cewa lallai babu tsoron wani abin ƙi da zai same su, ba kuma sa baƙin-ciki**

**saboda wani abu da suke so da ya kuɓuce masu. Fuskokin shahidai suna walƙiya saboda baiwar da Allah ya yi masu na ni'imar shahada, da ni'imar aljanna, da babban karramawar da aka yi masu, lallai shi Allah ba ya tozartar da ladan muminai)** [Ali Imran: 169 – 171], haka mai mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Kada ku soma ku kira wanda aka kashe shi a wajen ɗaukaka kalmar Allah da sunan "matacce", a'a, rayayyu ne su, ku ne dai ba ku sani ba)** [al- Baƙra: 154].

Lallai shahada tana da surori masu yawa, a cikin waɗanda suka fi girma da daraja akwai: shahada wajen bai wa ƙasa kariya, ta hanyar sadaukar da kai, da kiyaye turɓayar ƙasa, da bai wa 'yan ƙasa kariya, saboda neman yardar Allah mai girma da buwaya, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda aka kashe shi wajen kare dukiyarsa shahidi ne, wanda aka kashe shi wajen kare iyalansa, ko wajen kare ransa, ko wajen kare addininsa, to lallai shahidi ne shi),** wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) sai ya ce: Ya Manzon Allah, ya kake gani idan wani mutum ya zo yana son ya ƙwace mini dukiya ta? Sai ya ce: **(Kada ka ba shi dukiyarka)**, sai ya ce: idan ya yaƙe ni fa?, sai ya ce: **(Ka yaƙe shi)**, sai ya ce: to idan ya kashe ni fa?, sai ya ce: **(Ka zama shahidi)**, sai ya ce: idan na kashe shi fa?, sai ya ce: **(Ya shiga wuta)**.

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu

Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai an shar'anta yin yaƙi ne a Musulunci saboda hana zalunci da ta'addanci, shi addinin Musulunci ba yana rajin shiga cikin yaƙi da zubar da jini ba ne, hasali ma addinin Musulunci a duk sanda ya sami wata kafa ta hana faruwar yaƙi yana binta ya yi aiki da ita, saboda shi yaƙi a cikin Musulunci yana da iyaka da ƙunci, bayan kuma sharuɗɗa da suke yi masa tarnaƙi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai an yi wa waɗanda ake yaƙarsu saboda zalunci izinin su mayar da martani saboda bai wa kansu kariya, kuma tabbas Allah mai cikakken iko ne akan ya ba su nasara)** [al- Hajji: 39], haka ma Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Jure wa wahala wajen yin masa biyayya na daga cikin tsoron Allah, kuma abu mafi tsananin wahala a zuciya shi ne yaƙar maƙiya Allah, amma idan suka yi maku ta'addanci ku yaƙi waɗannan masu ta'addancin, tabbas an yi maku izini na mayar da martanin wannan ta'addanci nasu, sai dai fa ku kada ku fara yi masu ta'addanaci, ko ku kashe wanda ba ya yaƙi, ba kuma shi da wani ilimi akan yaƙi, lallai Allah ba ya son masu ta'addanci)** [al- Baƙra: 190], haka ma Allah mai girma da buwaya yana cewa: **(Idan maƙiya suka karkata daga barin ɓangaren yaƙi zuwa ɓangaren zaman lafiya, to ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) kai ma ka karkata zuwa ga zaman lafiya, saboda da ma can ba yaƙi ne manufa akan kansa ba, manufarka ita ce yin amfani da yaƙi saboda kare kai daga zalunci, da fito na fito da kiranka da suke yi. Saboda haka, ka amshi tayin zaman lafiyar da suka karkata zuwa gare shi, ka dogara ga Allah, kada ka ji tsoron ƙulle- ƙulle da makirce – makircensu, lallai Allah mai girma da ɗaukaka yana**

**cikakken jin abubuwan da suke kitsawa, yana kuma da cikakkiyar masaniya da abubuwan da suke ƙullawa, babu wani abu da yake iya ɓuya a gare shi)** [al- Anfal: 61], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Kada ku yi burin haɗuwa da maƙiyi, ku nemi sauƙi a wurin Allah, amma idan har kun haɗu to ku dage ku yi haƙuri)**.

Hasali ma addinin Musulunci a cikin yaƙin da mayar da martani ne akan zalunci da ta'addanci, ya hana duk wani abu da zai kai zuwa ga ɓarna da lalata abubuwan da aka gina, haka ma sahabban Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) sukan yi wa jagorori da kwamandojinsu wasici da kada su kuskura su sare bishiya, kada kuma su ƙona shuka, kada su auka wa manoma da suke a gonakinsu, kada kuma su auka wa masu bauta da suke a wuraren bautansu, kada su kashe mata, ko ƙananan yara, ko tsofaffi marasa ƙarfi, matuƙar dai ba sun shiga cikin yaƙin ne ana yi da su ba.

Lallai muna matuƙar buƙatar mu kasance a sahun masu kawo zaman lafiya da gina ƙasa, ba sahun masu rusa ƙasa da lalata kayan ƙasa, da na jama'a ba, duk inda yake akwai kira zuwa ga zaman lafiya, da gina ƙasa da raya ta, to lallai nan ne ya yi daidai da ingantaccen karantarwar addinai, duk kuma abin da yake kira zuwa ga kisa da lalata ƙasa gami da rusa ta, to lallai waɗannan abubuwa sun yi hannun- riga da dukan addinan Allah, hasali ma sun yi hannun- riga da kyawawan ɗabi'un mutuntaka da na abubuwan da aka saba da su na yarjejeniya da dokokin ƙasa da ƙasa; abin da yake buƙatar gaba ɗayanmu mu haɗu wajen tabbatar da duk wata ma'ana na zaman lafiya, mu kuma ƙalubalanci masu kira zuwa ga yaƙe- yaƙe da lalata al'amurra; za

mu yi haka ne saboda ɗan Adam ya sami cikakken tsaro da zaman lafiya a duk inda yake.

**Ya Allah Ubangiji ka kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashe daga dukan abubuwan ƙi, ka dawwamar mana da ni'imomin aminci da tsaro.**